# Ka Rera Waƙar Gaba Gaɗi

**Karanta Zabura 27:6.** Dauda yana son waƙa sosai kuma yana yawan rera waƙar yabo ga Jehobah. Da yawa daga cikin waƙoƙin sun taimaka masa ya yi gaba gaɗi. Rera waƙa za ta iya taimaka maka ka yi gaba gaɗi!

Ka karanta waƙar nan "Ka Ba Mu Karfin Zuciya." Waɗanne dalilai ne wannan waƙa ta ba mu na yin ƙarfin zuciya? Ka haddace waƙar nan kuma ku rera ta tare a matsayin iyali.

NINKA BIYU



WAƘA TA 137

## Ka Ba Mu Karfin Zuciya

(Ayyukan Manzanni 4:29)

1. Sa'ad da muke wa'azi,
Muna shelar sunanka,
Mutane suna sukār mu
Suna so mu ji kunya.
Maimakon mu tsorata,
Kai za mu yi wa biyayya.
Muna roƙo ba mu ruhunka;
Ya Jehobah, ji roƙonmu.

(AMSHI)

Ka ba mu ƙarfin zuciya;
Sa'da muke wa'azi.
Ba mu gaba gaɗi kuma
Don mu gaya wa kowa.
Armageddon fa ya kusa,
Amma kafin wannan rana,
Ka ba mu ƙarfin zuciya.
Muna roƙo.

2. Ko da mukan yi fargaba,
Ka san mu turɓaya ne.
Ka ce za ka taimake mu
Mun dogara gare ka.
Ka ɗauki mataki kan
Duk masu tsananta mana.
Ba dukanmu ƙarfin zuciya
Don mu sanar da sunan ka.

(AMSHI)



www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania